Ya Allah Ka kareni azabarKa ranar da zaKa tara ko zaka tashi bayinKa

Huzaifa Ibnul Yaman -Allah Ya yarda da shi -: Cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan ya yi nufin yin bacci yana sanya hannunsa ƙarƙashin kansa, sannan ya ce: «Ya Allah Ka kareni azabarKa ranar da zaKa tara ko zaka tashi bayinKa».

[Ingantacce ne] [Tirmizi ne ya ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan ya kwanta dan yayi barci, sai ya shimfiɗa hannunsa na dama kuma ya sanya kundukukinsa (kumatunsa)na dama akansa, sai ya ce: «Ya Allah» Ubangijina «Ka kareni» Ka kiyayeni daga «azabarKa» da uƙubarKa «ranar da zaKa tara ko zaKa tashi bayinKa» a ranar hisabi, ranar alƙiyama.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/6167